| JUMHURIYYAR MISRA TA LARABAWA | 5 Muharram, 1443 |
| --- | --- |
| MA'AIKATAR ADDININ MUSULUNCI | 13 Ogusta, 2021 |

(1)

## YIN TSARI, DA MIKA AYYUKA GA WAƊANDA SUKA CANCANTA SUNA CIKIN DARUSSAN DA HIJIRAR MANZON ALLAH TAKE KOYARWA..

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((In ma ba ku taimaka wa Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa wa alihi wa sallam) ba, to ku sani tabbas Allah ya riga ya taimake shi a lokacin da kafirai suka fitar da shi daga garin Makka su biyu, lokacin da suke cikin kogo da yake faɗa wa abokinsa cewa: kada ka damu, lallai Allah yana tare da mu, sai Allah ya saukar masa da natsuwa, ya kuma ƙarfafe shi da rundunar da ba ku iya ganinta, ya kuma sanya kalmar kafirai ta zamo a ƙasa, lallai kalmar Allah ita ce a sama, tabbas Allah cikakken mabuwayi ne, mai kuma cikakkiyar hikima))** **[at- Tauba: 40]**, Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya, ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabin mu Muhammad bawansa ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai hijirar da Annabi Muhammad (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya yi daga garin Makka zuwa garin Madina cike take da darussa, gami da izina, lallai hijirar wata babbar gaɓa ce da ta kawo sauyi a tarihin Musulunci, a

cikin muhimman darussan da suka kamata mu tsaya mu duba su da kyau akwai: kyautata tsari, da kuma bi dinƙin-diƙin wajen ajiye komai na wannan tafiya mai albarka a inda ya dace da shi, lallai yin tsari hanya ne na kauce wa kowace irin matsala, kuma abu ne da ake matuƙar buƙatarsa muddin ana buƙatar a sami nasara, za mu gane haka a fili ne idan muka kalli irin yanda Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya samar da abin hawa guda biyu saboda wannan tafiya mai albarka, ya kuma zaɓi Sayyiduna Abubakar al- Siddiƙ (Allah ya ƙara yarda da shi) domin ya zamo abokin tafiyarsa, haka ma ya zaɓi dare ne a matsayin lokacin da ya fi dacewa a fita daga garin Makka.

Haka ma duk wanda ya lura da abubuwan da suka faru a lokacin hijira mai albarka zai ga irin yanda Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya rarraba wa mutane ayyuka, da rawar da kowa zai taka, a cikin wani yanayi na ƙwarewa da gwaninta, dubi yanda ya umurci Sayyiduna Aliyu Bn Abuɗalib (Allah ya ƙara yarda da shi) da ya kwanta a shimfiɗarsa, ya lulluɓa da mayafinsa; saboda ya mayar wa mutane da amanoni, gami da ajiye- ajiyen da suka ba shi, bugu da ƙari kuma, hakan zai shagaltar mushrikai, ya hana su yin saurin bin sawun Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) lokacin da zai fita.

Lallai za mu fahimci irin yanda Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya muhimmanta yin tsari, da aiki da sababi a cikin wannan tafiya ta hijira mai albarka lokacin

da ya zo wurin sahabinsa Sayyiduna Abubakar (Allah ya ƙara yarda da shi) a lokacin da bai saba zuwa masa a irinsa ba; saboda su fita su kama hanyarsu ta yin hijira, bayan ya ɗaura wa Sayyiduna Abdullahi Bn Abubakar (Allah ya ƙara yarda da shi) alhakin bibiyan labarun Ƙuraishawa, ya binciko masu irin makircin da suke ƙulla wa wannan karafta ta hijira, inda yake zuwa da rana ya nemo masu labari game da makircin da Ƙuraishawa suke ƙullawa, da daddare kuma ya tafi ya kwana tare da Annabi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da sahabinsa a cikin kogo, sannan da safe ya sake dawowa garin Makka.

Haka ma Sayyiduna Abubakar (Allah ya ƙara yarda da shi) ya tsara yanda hadiminsa Amir Bn Fuhaira (Allah ya ƙara yarda da shi) zai rinƙa kawo masu abinci ta hanyar yin kiwon tumakinsa a kusa da kogon, saboda sawun tumakinsa su share sawun Abdullahi Bn Abubakar, bayan kuma duka wannan ga Sayyida Asma'u Bint Abubakar (Allah ya ƙara yarda da ita) nan, wadda aka fi saninta da suna "Zatin Niɗaƙaini" tana yin takakka zuwa Kogon Saur ɗauke da abinci za ta kai wa Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da sahabinsa (Allah ya ƙara yarda da shi).

***

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga cikamakin Annabawa da Manzanni, shugabanmu Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Lallai a cikin muhimman darussa a hijirar Annabi mai daraja akwai: miƙa ayyuka ga waɗanda suka cancanta, kowa gwargwadon ikon da yake da shi, inda Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), da sahabinsa Sayyiduna Abubakar (Allah ya ƙara yarda da shi) suka yi jinga da wani mutumi da zai yi masu jagora a hanyarsu ta zuwa Madina, wadda take hanya ce ma cike da kwazazzabai, da tudu da kwari, ba a miƙe take ba, wannan mutumi kuwa shi ne Abdullahi Bn Uraiƙiɗ, shi ɗin fa ba Musulmi ba ne, amma duk da haka Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya zaɓe shi; saboda (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya yi imani da gabatar da wanda ya cancanta, da yin amfani da ƙwarewa a cikin komai, ba tare da la'akari da bambancin tunani, ko ra'ayi, kai har ma bambancin addini ba, an ruwaito Hadisi daga Ummul muminina A'isha (Allah ya ƙara yarda da ita) ta ce: Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), da Abubakar sun yi jinga da wani mutum.. ɗan jagora.. suka amince masa, suka miƙa masa abin hawansu, su yi alƙawarin ya kawo masu abin hawan nasu zuwa Kogon Sauri bayan darare uku, watau a safiyar na ukun, sai Amir Bn Fuhaira ya tafi tare da su a matsayin ɗan jagora, sai ya ja su ta hanyar gaɓar kogi).

Duka wannan abu yana karantar da mu wajibcin yin aiki da sababi, da kuma gabatar da ingantaccen tsari, da kuma yin amfani da kwararru da suka cancanta a cikin komai, musamman a cikin manya abubuwa, kuma lallai hakan ba

wai yana nufin ba a dogara da Allah mai girma da buwaya ba ne, domin da Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya so, da ya roƙi Allah Mai girma da ɗaukaka ya sanya Buraƙa ta ɗauke shi daga Makka zuwa Madina, kuma duk da irin yanda (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yake da cikakken sanin Ubangijinsa, da kuma siƙar da yake da ita na cewa lallai zai taimake shi- amma bai yi hakan ba, sai ya karantar da mu yanda za mu yi aiki da sababi, ta yanda za mu shirya, mu tsara komai da komai, sannan a ƙarshe mu bar wa Allah mabuwayi natija da sakamako, wanda shi ne yake samar da shi yanda yake so, za mu fahimci haka ƙarara lokacin da Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ɗauki dukan matakan da za su sanya a yi nasara, sannan a lokacin da mushrikai suke bibiyansu ya ce wa sahabinsa: **(Kada ka damu, lallai Allah yana tare da mu)** sai kuwa Allah Maɗaukakin Sarki ya saka masa da cewa: **(Sai Allah ya saukar masa da natsuwa, ya kuma ƙarfafe shi da rundunar da ba ku iya ganinta, ya kuma sanya kalmar kafirai ta zamo a ƙasa, lallai kalmar Allah ita ce a sama, tabbas Allah cikakken mabuwayi ne, mai kuma cikakkiyar hikima))** **[at- Tauba: 40].**

Ya Allah Ubangiji muna roƙon ka azurta mu da koyi da Annabinka (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam).